Da farko sunana Najaatu Ado Haruna ,Ina karatu a jami'ar Yusuf Maitama Sule wacce take a kofar Nassarawa, wato gidan Ado Bayero, ina matakina farko wato (level one). Kuma ina karanta International Studies. lambar karatuna itace UG17INT1026

inaso nayi magana akan hanyarmu data damemu, wacce ta tashi daga kinsgarden xuwa tudun murtala wadda maigirma gwamnan kano, Dr Abdullahi umar ganduje yabada kwangilarta kimanin shekara uku dasu kawuce Wannan hanya ta hada unguwanni da dama Wanda kasancewarta haka yanacimana tuwo akwarya, domin yawancin mu mazauna wadannan yan makaranta masu anfani da wannana hanya mukansha wahalar samun abin hawa, saboda yawan rashin kyan hanyar ababen hawan basa son bita hanyar nan. Haka ma yayin fita makaranta ko aiki gamasu zuwa aiki ko ga yan kasuwa. Hakama yayin dawo yan adaidaita sahu basa kaimu har, unguwannin mu saidai su barmu a kinsgarden saboda lalacewar hanyar. Aikin yatsaya cik,kumayan kwangilar sun daina komai na aikin awajen, kusanma ince sun kwashe kayayyan akinsu, sakamakon gwamnati tayi halin ko inkula da aikin. Haryau basu cigaba da aikin ba sai kura da take damun mu. Masu shaguna damasu abinci suma sunta kokawa kwarai akan halin da hanyar nan take ciki. Ba wannanne bama abin ban haushin, shine yadda mutane suke kamuwa da cututtuka, kamar Asma, mashako, Tarin Fuka da dai sauran cututtukan da kura ke haddasawa. Kuma gashi sau da dama motoci suna makalewa akan titin, sai kuma sunyi kwana kusan biyu kafi nan cire motar daga ramin nan. gashi kuma yanxu sanyi yashigo, kura duk ta addabe mu musam manma wadanda suke daf da hanyar. Mutane da dama yanxu basu son su shiga brigade saboda jar kasar da take wajen Nan kura duk ta Bata su kuma tashege musu i'danowa.
A gaskiya mutanan wadannan unguwarku data hada, king'sgarden, Layin pampo, kwanar kifi, Yan kaji, Sarkin fawa, Asibitin gwagwarwa, Bakin kasuwar brigade, Tudun wada, Tsamiya, Da kuma Tudun murtala muna cikin wani Hali mara Dadi.gwagwarwa Wanda shima hanyar tahada dashi Ana samun matsla sosai kafin a samu a kawo Mara lafiya,ma xaunan wandannan unguwanni sun ko matuka saboda yarda gwamnati tayi watsi da aikin. dai alamarin yacitura.Munarokon  gwamnan jahar kano daya duba Allah yakawo mana dauki mu mutanen wanan unguwar, kasancewar lokacin zabe yaga bato idan akabarmu ahaka lokaci yakure hankalin gwamnati zai koma kan harkar siyasa shikenan mu mutanan wadannan unguwanni saidai hakuri kenan, saboda hankalin zai koma wasu sababbin ayyuka namu Kuma  yazama tsoho.

Sunayen unguwananin da abun yashafa sun hada da - kinsgarden, Dorawa, Kwanar kifi yankaji, gidan sarkin fawa, Kwanar tudun wada, har zuwa tudun murtala.